Mun tafi mu taro Annabi SAW tare da Yara a Thaniyat Al-Wadaa

An rawaito daga Al-Sa'ib Bn Yazid -Allah ya yarda da shi- yace: "Yayin da Annabi SAW ya iso Madina- daga yakin Tabuka Mutane sun tare sai na tare shi tare da Yara, kuma a cikin wata Riwayar ya ce:"Mun tafi mu taro Annabi SAW tare da Yara a Thaniyat Al-Wadaa"

[Ingantacce ne duka Riwayoyin nasa guda biyun] [Buhari ne ya rawaito shi - Abu Daud Ya Rawaito shi]

Al-Sa'ib ya bada Labarin cewa shi yayin da Annabi ya SAW ya iso Madina tare da Sahabbansa suna masu dawowa daga yakin Tabuka sun futo don tarbarsu a Thaniyat Al-wadaa, kuma ita wani guri ne daf da Madina, kuma wannan don dauke musu kewa ne da dadada musu, da kuma kwadaitarwa ga wadanda basu futa yakin ba

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/6386